**<u>Tambayoyin Tattaunawa Bayan Dubawan Finafinai na "VOTE NOT FIGHT" (kada kuri'a yasa fada)</u>**

Finafinai gajeru da kuka kalla, an yi su ne don tattaunawa batun al'amurorin da suka taso. Ku tattauna batun su a cikin **k**ananan **k**ungiyoyin ku.

Tambayoyin tattaunawa, mafi kyau sune wa**d**an da suke nan:

- Da amsosi wa**d**an da dole ne sai da dogon bayani, babu amsan "A" ko "A'a".
- Da suke neman dalilin mesa abubuwa suke nan, ko ya kamata suke nan
- Suke ganin al'amurori daga ra'ayoyi masu yawa
- Suke jawo tunani
- Suke jawo sha'awar mutane

Mun bayar da misalai, amma za ku iya **k**ara naku.

**<u>MISALAI</u>**

**TASHIN HANKALIN LOKACIN YIN ZABE**

1. Ka ta**b**a ganin wurin da a ka yi tashin hankali a lokachin za**b**e?
2. A ganin ku, mesa mutane suke yin tashin hankali a wurin yin za**b**e?
3. A ganin ku, yaya halin 'yan Najeriya yake game da tashin hankali a lokachin za**b**e?
4. Waye tashin hankalin yafi shafa?
5. Waye tashin hankalin da hargitsin yafi amfana?
6. Me zamu iya yi, a matsanin mu na 'yan **k**asa, mu tsayar da tashin hankali kafin ta fara?
7. Me Gwamnati za ta iya yi don hana tashin hankalin?
8. Akwai alamun tashin hankali?
9. Idan har tashin hankali ta zo, menene abun yi, mafi muhimmanci?
10. Menene amfanin yin za**b**e marasa tashin hankali?

**KATIN ZABE (PVC) / FITOWAN ZABE**

1. Me yasa muke da katin za**b**e?
2. Me yasa ne wai mantawa da katin zabe ba wuya?
3. Ina ne za ku iya ajiye katin za**b**en ku don ku tuna ku kawo shi wurin zabe?
4. Yaya kuka yi kuka same katin za**b**en ku?

5. Yaya za'a yi za**b**e da a ce babu mai katin za**b**e?
6. Samun katin za**b**e yana sa mutane su fito yin za**b**e, ko baya yi?
7. Menene babban abun motsawa, dake karfafa mutane yin zabe a ranan yin za**b**e?
8. Menene wasu dalilai da mutane suke bayar wa don kada su yi za**b**e?
9. Yaya za'a iya shawo kan mutane da kyau, don su fito su yi za**b**e?
10. Waye ya fi amfana idan mutane ka**d**an su ka fito yin za**b**e?

**SAYAR DA** K**URI'A**

1. Yaushe ne, kuma me yasa ka ta**b**a sayar da **k**uri'an ka?
2. Nawa ne darajan **k**uri'an ku a tunanin ku?
3. Me yasa sayar da **k**urian ku bashi da kyau?
4. Shin, mai sayar da **k**uri'a ya yar da 'yancin sa na ri**k**e 'yan siyasa su yi aiki idan suka hau mulki?
5. Daga ina ku**d**in siyan **k**uri'a take fito wa?
6. Yaya 'yan siyasa suke tabbatarwa mutane sun za**b**e su bayan sun biya su?
7. Wanne za ku fi so – sayar da **k**uri'a naira millon, ko kuma 'yan siyasa su cika al**k**awuran za**b**en da su ka yi?
8. Banda **k**udi, me 'yan siyasa suke amfani da gurin siyan **k**uri'a?
9. Kuna gani yana da kyau cewa wai da mai sayan **k**uri'a, da mai sayar wa sun sa**b**a wa doka?
10. Me za'a iya a kawo karshen sayar da **k**uri'a?

**ZA**B**E TA KOWA CE**

1. Kuna yin zabe? Kuna da niyyan yin zaben nan gaba? (Idan baza ku yi ba, me ya sa?)
2. Meye abu daya da zai iya saka ku kada ku jefa **k**uri'a a ranan zabe?
3. A Najeriya, wane **k**unguyoyi kuke gani suke samun wuyan zuwa yin zabe?
4. Me kuke gani za'a iya yi don a gani ce wa ko wane **k**ungiya a jahar sun fito sun yi zabe?
5. Kun san mai fama da rashin lafiya da ya ta**b**a yin za**b**e? Yaya za**b**en ya kasance?

6. Kun ta**b**a gani an yi rashin adalcin ga zuwa mai fama da rashin lafiya, ko tsoho a wurin za**b**e?
7. Nisan wurin zabe ya ta**b**a zama matsala maku a ranan za**b**e? (Idan haka ne, me kuka yi?)
8. Me yasa kuke gani wa**d**an su matsalolin suke nan har yanzu?
9. Me kuke gani za'a iya yi, don yin za**b**e ta yi sau**k**i ma kowa?
10. Yaya za ka iya taimakon wani mai fama da wata illa ko rashin lafiya, a ranan zabe?

**LABARUN** K**ARYA (FAKE NEWS)**

1. Yaya za ku yi bayanin "labarun **k**arya"?
2. Me nene bambancin bayanin da ba daidai ba da "labarun **k**arya"?
3. Me yasa labarun **k**arya su ka zama wanan irin babban matsala?
4. Kuna gani an ta**b**a cinku da labarun karya?
5. Yanzu za ku iya tunawa da labarin karya da kuka ta**b**a yadda da? Me yasa kuka yadda da shi?
6. Wa ye yaduwan labarun **k**arya yafi amfana?
7. Wa ye mai rike nauyin kulawa da labarun **k**arya?
8. Me Gwamnati za ta iya yi don hana yaduwan labarun karya?
9. Menene abun fari da ya kamata ku tambayi kan ku idan kuka karanta labarin da baku yadda da shi ba?
10. Yaya ne hanya mai inganci da kyau da za ku iya nuna ma mutum ce wa labarun da suka yadda da **k**arya ne?